Appendix B Hausa Roman script poems

Hadijatu - A Poem on the Mahdi *Wa'kar Mahdi* originally in Fulfulde.

1 Na gode Allah bisa ga wadda anka yi ni Musulma domin bi'da agaji
2 Na sallama ga Muhammadu ga'ba'be da arlayenai da mutuum duk wanda a soyaye
3 Nufina in fa'di, maganar mahadi, in kawo abinda anaka fa'di, anka kawo.
4 Hanyar ta taro sunka game, ba 'dan Askiya'u ba don ka lura
5 Ba haka ne ba, babu wannan hanyarsu ya sa'ba ma magananga
6 Domin hadisai sun gabata bisa zakuwartai har sun hukunta
7 Da yawa mutane sunk ace ana kashfi bisa ga zakuwartai, haka sunka ambata
8 Saura guda daga cikinsu, ko saura da hu'dunsu, ko saura da shida wasu sun ce guda kuma wasansu sun ce goma sha 'daya
9 Ko ka ha'da ashirin da 'daya, babu abinda ya rage ko 'daya
10 Sun fadi 'dari uku bisa ga dubu zakuwartai haka anka inganta shi
11 Anka fa'di talatin aka sabka sheshi haifuwartsa sittin adda saura su cika
12 Cikarsu zakuwartai wa'danda sunka ce da shekira arba'in shika zakuwar
13 Wasu ko talatin sunka fa'di anka haifeshi da 'dari haka anka ambatta
14 Sa'annan kuma da sittin aka daukartai ko saba'in aka dauka shi
15 Wasu ko sun ce kuma ko talatin da biyar zakuwartai ta nuna
16 An biyar ko saba'in da biyart anka ambatta
17 Wasu kuma saba'in da shida sunka fa'di zakuwartai sittin da shida ta zamo
18 Wasunsu maganar ta biyu sun fa'di saba'in da shida kuma zakuwartai ka lura abinda nif fa'di
19 Wasunsu kuma sun fadi arba'in anka jisai zakuwartai saba'in anka ayana
20 Ko ko tamanin in sun cika bisa ga masu nuni suna ambatta
21 Yabanin zakuwartai akwai fitinu da yawa ga kashe kashin kanu bisa ga zamba
22 Da ragancewa mutanen sham da abokan an yi fa'da fadan su har a rinjayesu
23 Da kamma wata azumi, da shi da rana an fa'de su
24 Da rabuwar rana shina cikin alamu wanda anka fa'di
25 Da bayanar da tauraro da babbar wutsiya wutsiyar nan mai haske ta
26 Kuma da fitar wuta cikin sammai mai yawan haske
27 Da rinjiyar mutanen Turku ga Misarawa da yawansu gari gari suna wahalarasuwa
28 Da fitar 'bayi ga da'a ubangidansu da damama shi zuwa rai
29 Da firtar da'a yara, da dogon rani an ambaci wa'dannan abubuwa
30 Saura wa'danda a kusa, da fitowarsu ko fitar zafi ka lura da wannan…

Maryam - The Scattering of the Hausa *Fa'dar Shehu Kan Watsewar Hausa*

1 Musulmi ku kai 'karammu inda Muhammadu, zama shi ka ceto ran da babu wurin gudu
2 Mu bar kafiri da munafiku shi da hasidu zama su Kuware sukai na sun kai ga Masjidu
3 Ku san Bello ya amsa ga Shehu Mujaddidi batun Hausa na tashi a waste a bar ta du

4 Muna tafiya lau lafiya har mu zo Masar mu zaman a wajjan dama inda Mujaddidu
5 Ma'ki ji shina nan ba ruwa baa abin dake rabo nai hasaran lahira nana bai gudu
6 Sa'an nan mu zo har 'Durisinina anka ce, batuna ha'ki'kan gaskiya na mu'ayyidu
7 Irin Shehu ad da tafiyan nan ku tabbata ku tanye shi in dai mu ganai wanga Sayyidu
8 Tagomas na Shehu da arziki duk suna garai zama jama'a tai rukka'un na da sujjadu
9 Garin duk da sunka biya ana marhabin da su zama su waliyyai na na Allah da Ahmadu
10 A 'dauke ruwa bayan Musulmin ga sun wuce guladen ga duk su 'kafe Kuwara ta zam tudu
11 Da giwa da zaki babu kura cikin dawa bale ka ga tsuntsu ko 'kuje babu wahidu
12 Ri'ke mini ya zam taulafina Muhammadu ina son ka ha'k'kan ka sani bar taraddudu
13 Salatun da taslimun su dawwama hakaze su rakki salamun Rabbu har inda Ahmadu.
Tamat Bihamdillahi

<u>Maryam - On Becoming Imam *Limanci* original in Fulfulde</u>

1 Allah nike gode ma, wanda a gaba a bi shi, ku bi muna Muhammadu, an gabatarshi
2 Kowa ya yi limanci, anka bi shi, shi ya yi koyi (da Annabi), ku bi nuna Sahabi, an sa su gaba
3 Mutum goma sha tar aba su limanci, cikinsu shida an haramtarsu
4 Wa'dansu daga cikin wa'danda da sunka rage, an yi sa'baninsu bayan haka wa'danda sunka rage, an 'ki su
5 Wanda shigatai ya mutu, da mai yankaka ga'ba, hakanan mai kuraje shi an 'ki shi
6 Haka nan 'dan zina da bawa haka nan mai yin boli hakanan mai yin kasha
7 Haka nan wanda ya zo ba a san halinsa ba haka nan daddakake haka nan wanda ba'ayi kwido ba
8 Hakanan mutuum irin wanda mutane ba su so
9 Hakanan wanda bai zan namiji ba bai zam mace ba, an haramta shi
10 Hakanan kafiri, hakanan mace, hakanan mahaukaci, haka nana yaro duk haramce
11 Bayan haka nan, wa'danda anka halalta za su fa'di don mu san su
12 Mai karima talitta, haka nan makaho, haka nan mai kuturu kuma haka wa'danda ana saba ga fanoni halal
13 Haka nan wanda bai san abinda ke gyaran Sallah ba, haka nan fasi'ki na ga'bai, an yo hilafa
14 Bayan wannan, wa'danda ake so zamu fadi don mu san su, don an so su
15 Wanda ya fi kowa iya hadisi, mai kyawon karatu, haka nana tsoron Allah, haka nan, ibada, an so shi
16 Mai kyawon tufa, mai kyawon ga'bai, haka nan 'dan dange mai yawan uwa, da yawa an so shi
17 Haka nan Sarkin 'kasa da wanda adda gida da za a yi Sallah ciki, haka nan mai tsereran ga'bai
18 Wa'danda anka haramta su yi limanci, in su yi, ba bi, kowa ya bi su sallartai ta 'baci

19 Wa'danda anka ambatta suna limanci in ba a samu wasu ba, in an samu a bar su
20 Wa'danada sunka halalta in sun yi limanci, Sallah ta yi kyau, bake duk wa'danda anka so, su an so su.

Composed by Ilyasu b. Abdullahi b. Abdulkadir b. Shehu, great grandson of the Shehu, killed at Anka in the 1830s - A Poem about Maryam *Wa'kar Maryam*

1 Ina yin godiya ga Ubangijina garin nika tamaha da dare da rana.
2 Muhammadu ya fi kowa babu shakka ga talikai ga Rabbin alamina
3 Ta baraka Rabbana Sarkin sarauta ka bar muna Maryam kai mai janana
4 Ba ta rika agaji jama'a musulmi Talakawa, zumai ko wani na
5 Ka ba ta fa lafiya sarkin sarauta ku ce amin mu yo murna zumaina
6 Zama ihisaniya ba zam gare mu ga musulunci da addin da sunna
7 Dai hi daukaka ta ta sami afuwa diya Uthman mai son 'dan Amina
8 Maza riga da mata nansu zanna ta ba su bukinsu domin 'dan Amina
9 Da malamai, da masu zawa jihadi tana ba musulmina da muminina
10 Wadansu maza dawaki sunka samu ilahi 'kara ba ta dare da rana
11 Wurin mata daban shiki din ku ji shi, tana wa'azi gare su dare da rana.
12 Ga hanya annabimu gare ta ta 'bi gare ta mujaddid ya biya da sunna
13 Malaiku na Allah niyi roko na sarki wanda ya yi dare da rana
14 Ilahi karasa mata dau'karga dalilin wanda ya zauna Madina
15 Da alfarma ta makka da daiba rawla da alfarman jama'a kadirina
16 Da alfarma sahabai har waliyyai ka bar muna Maryam don maiu Madina
17 Da alfarma ta jikokin Muhamman Huassain Hassan Amirul Muminina
18 Bukinta na dunya sarki cika shi da barzahin lahira har shan jinana
19 Mutane 'dan Adam a mu bar ayyuka na sa'bo don mu tuba dare da rana
20 Dada na cika na goda Allah ina yin a salahu da 'dan Amina
21 Idan an tambaya shin na yi wa'ka ku ce Ilyasu mai son 'dan Amina.

Aishatu, daughter of Abdullahi, Asma'u's niece Prayer *Wa'kar Sallah*

1 Na gode Allah ma'abucin tsira, na sallama Ahmadu mai babban matsayi
2 Na sallama ga sahabbai da arlaye da taba'ina, mutanen cikawa
3 Kowanin mu ya damre aniya da gyara sallah don in an amsa abu duk ya yi kyau
4 Saboda in an diba sallah mutuum anka amsheta, in ba a amsa ba, ibada duka ta fa'di
5 Sanin abinda ke gyaran sallah, sujuda ta kabla
6 Wanda ya bar sura guda sujuda 'kabla amma bisa ga abinda anka amso ga mallami
7 Inda anka bar kabbarori biyu, sujuda 'kabla an yi hukumci da ita
8 Wanda ya 'boye karatu wurin bayyanawa sujuda 'kabla anka aza mishi
9 Haka nan sami Allahu in anka bari har sau biyu, 'kabla anka aza mai
10 Haka nan atafiyatu wanda ya bar shi ba da 'kabla a bisa gare shi
11 Zaman tsaka in anka mance shi, sujuda 'kabla anka aza mai
12 Fatiha in an bar ayarta guda, 'kabla zai kawo shi ida sallah
13 'Kabla ya kare maganar ba'ada ta bayan Sallah abinda ya jawo shi in gwada ma
14 Mai sallah in ya yi sallama tsakanata ba'ada shike bayan ya yi sallama
15 Wanda ya kara ba'ada shike, baya garesu shika basuwa

16 Wanda bai sani ba abinda ya yi sallah ba'ada shike baya da ya yi sallama
17 Wanda ya yi fatiha biyu, ba'ada shike shi ko, bayan ya yi sallama
18 Zaman tsaka wanda ya tashi garai har ya rabu da 'kasa sai ya tuna, ba'ada shike
19 Ba'adu in ta kam ma, yi 'ko'kari ka kawo in ka yi shakka ko yaushe ba'ada kake
20 In ka mance 'kabla, ka yo ba'ada kada ka jinkirta, in ka jinkirta, sai wata Sallah
21 Mu fata yin wa'ka don a kula ga ayyukan sallah
22 Na cika, na gode Allah, na yi sallama ga Ahmadu mai babban matsayi.

Hussaina – Joy at the Victory over the Chief of Ningi Translated from Fulfulde into Hausa roman by Ibrahim Sulaiman

1 Muna gode Sarki Jalla ya yi mana taimako da ya ba mu nasara, mun yi murna da godiya
2 Muna yin sallati ga Annabinmu da sallama da allai sahabai tabi'ina da mai biba
3 Dada zani wa'kata ta murna farin ciki Haruna 'daya zuka anka koreshi 'dai'daya
4 Haruna da Ibru sune kumya ga duniya kaza lahira susha aza'basu mai wuya
5 Dada sumka yiwo gayya da faharinsu mai yawa su sheza suna fa ga Abdu sun fada 'dai'daya
6 Gatarshi nafari Haruna ya gudu nandanan da yaya da bardenai da tsatinsa kun jiya
7 Ashana wurin daga dubu anka karkashe dubu anka kaisu ga Abdu ya mika mikiya
8 Da kura tana murna tana 'kara dariya tana godiya nasara samari na gaskiya
9 Tsakani Rumufa da Janbu can anka karkarshe samarin Haruna fa summace babu ko 'daya
10 Awa nasara yaki ta daga da anka yiwo awa ta badar ta Jalla yabamu kun jiya
11 Idan sunka ga gaida Haruna shi tambaya da wane daga anka koremu daidaya
12 Suce masa Yusuf na uba nai shina gida fa sai ku baradai nai da kan minsa su daya
13 Fa su sunka kore Haruna sarkinmu na gida da shi da sarakin nai da bayinsa ka jiga
14 Dada ya shige dutse shina yin bakinciki Shina yin nadama wadda ba tada muriya
15 Kafid Haruna cikin duwatsu Ubangiji kaza ka da Ibru hal mutanensa ka iya
16 Musulmi mukuba mu bar ra'da'du da hazada mu zam duka ya'ya muzam duka ka 'daya
17 Idan munka tuba a babu nasa da daukaka bisa kafirai wannai da sunka ki gaskiya
18 Kasa zuciyammu ga yin jihadi Ubangiji ka karfafa Imani
19 Kabar muna sarki Abdu Jallah Ubangiji ka bashi yawar rai mun yi rokonka mun maya
20 Da albarkarkacin Shaihummu Ususmanu Fodiyo da ya yi Jihadi ya tsaya ga gaskiya
**21 Verse missing**
22 Ka bar muna ran 'ya Shehu Jalla Ubangiji kabata yawar rai mai yawa kai fa ka iya
23 Kabar muna kan Sarkin Muhammad Abubakar da jama'ar Musulmi duk mu zamna da lafiya
24 Ta'ala ka shafe mani zunnubai duk ka shafe kurakuran zama kai fa iya
25 Ka gafarta innata da 'ya'ya da 'yan uwa da sauran musulmi Jalla kai 'dai fa ka iya
26 Dada na cika Allah shi karba ina yabo da nitashi wa'ka yafa tayani kun jiya
27 Muna yin Sallati ga Annabinmu da sallama da Alai Sahabai Tabi'ina da manbiya.

Saudatu b. Alkalin Sokoto – Elegy for Sarkin Yamma, Hussaina's son circa 1936

1. Bismillahi za ni waka 'yan'uwa nai zani murthiya walilyyi mumini
2. Kuma na yi sallati ga Annabimmu Muhammadu har kuwa da allai da sahabai da ya bi
3. An littifafai adili na saliyi kuma malami shi abdin dayyani daya a ni ji
4. Ya san fa Allahu ya fa gaskanta shi duk ya ko bi sunna annabi dayani
5. Mai hankure waanaa ga Almari da duka shari da alheri sai shi she dayani
6. Na garda ma Fullani har mai yamma duk Na garda attahiru don dayyani
7. Na gaida ko bunu duk da Ali da Junaidu duk Na garda A'i'fa Amiru don Addini
8. Hayfe na sarkin yamma ali lana Allah shi gafarta ma'Aldiyin
9. Na gaida goggo ta Tajalidu mumini babban waluyyi na 'kaman 'kurani
10. Na gaida Nana diya ta'azilyijuta jiyaka na'abdu Allahi min Adiyinyi adini
11. Na garda toro Muhammadu har Bayero har Ahdamu da Hassan diyan Uthman
12. Sa'adu da yali sumu haiki 'katun haife na sarkin yamma shiyi usumani
13. Na gaida Basharu da Bubakar har Isa duk na gaida Shehu da
14. Na gaida Abbas Ahmadu 'dibgo akuma na gaida kinbal yabo mai Ali
15. Na gaida Hannatul malama har Yawdatu na gaida Fadima da mu Hafsatu jini
16. Na gaida mai'kari 'daan ummu da Aisha har yakanana sarudun da ya ni
17. Allah shi gafarta ma Bayero mu mini mai maslahane mai fasun 'kurani
18. Na gaida dabai da anto har haihanato na gaida 'diya da auta don Uthumanu
19. Saura fa jikokin Shehu Fodio saura ta kus bisa ko fa sun su'di
20. Hoho Amril Mumini Waziri ko sanunku umra'udu nako sanunku umaraunko sudani
21. Na gaida al'kali fa malam shaihuci ahabiiye 'dalibai Uthman
22. Fau ho honku mala sana malam sani fo sanonki da kufa malama sudni [saudi]

23. Kulum adadi yashuwa da tabsiri takai ga ta sa fa sudan fako dayyani

24. Allah ya ba da'da Fati ha'ksa duk shinka wa magari bayamal bishimali

25. Na gaida Hajara har Shaturu da Saudatu sannunku Saudatu sanu maidayani

26. Na gaida turai umma wala da ta garai har duda hasana tai uwa Ushmani

27. Na gaida Ilyasu fa da na jaliluna shi amakas kan 'kumamai il diyani

28. Nauyin tu fa fa abashi sundusu aharrin har abkarr har riafardayani